# BAYANI DON WAKILAI DA MARASA LAFIYA
## GWAJIN CRASH-3

| | |
|---|---|
| **Taken gwaji** | Tranexamic acid don magance raunin kwakwalwa mai tsanani ; gwajin canke mai sarrafawar maganin gwaje na duniya baki daya |
| **Lambar wurin gwaji** | |
| **Zubin takardar bayani** | 1.2 [Nijeriya] ; 06/09/2016 |

**Wannan asibiti ya shiga wani nazari na duniya baki daya don samo ingantacciyar hanyar warkar da raunin kai.**

*(Daya daga wadannan zabuka biyu ya shafe ka)*

(1) **A matsayin wakilin marar lafiya:** Wannan takarda tana bayar da bayani game da nazarin don taimaka maka ka zartas da shawara a madadin marar lafiyar.

(2) **A matsayin marar :** Bayan rauninka na kai, ka sami duk kulawar gaggawa da aka saba ga raunin kai wadda muke samarwa a wannan asibitin. Haka kuma an zartas da shawarar shigar ka cikin wani nazarin na duniya baki daya don samo ingantacciyar hanyar waraka ga raunin kai. Saboda raunin da ke jikinka ba lalle ne ka iya zartas da shawara da kanka ba amm yanzu da yake ka fara samun sauki, muna son yi maka bayani game da nazarin sannan mu tambaye ka ko kana son cigaba da kasancewa ciki.

**Kafin ka zartas da shawara, yana da muhimmanci ka san dalilin yin nazarin da kuma me ya kunsa. Karanta bayanin da ke kasa sannan ka yi tambayoyin da za ka yi kafin ka zartas da shawara. Wannan takarda tana bayanin dalilin da ya sa mu ke yin wannan nazari da kuma fayyace amfani da hatsarin shiga nazarin. Likita ko Ma'aikacin jinyar zai so ya tattauna da kai game da nazarin kuma zai amsa kowace tambaya da za ka yi.**

### 1) Mecece manufar wannan nazari?

A cikin wannan asibiti, ana yi wa marasa lafiya dake da rauni a kan su aikin gaggawa kamar yadda aka saba. Manufar wannan nazari shi ne don a samo ingantacciyar hanyar yin aiki sannan da saurin warkewa. Muna fatan cewa aikin warkarwa na nazarin (tranexamic acid) zai hana faruwa ko ya rage zubar jini zuwa cikin kai bayan faruwar rauni a kai wanda hakan zai kawo kyawawan sakamako. A gaba daya, babu wasu dalilan lafiya da ke cewa kar a baiwa marasa lafiya masu raunin kai tranexamic acid amma in likita ya ga cewa maganin bai da ce a irin halin yanayinka ba to ba za su hada da kai ciki ba [marar lafiya] a cikin nazari. Muna fatan aikin bada maganin zai yi matukar amfani fiye da illa amma dai ba mu gano haka ba.

### 2) Me ya sa aka zabe ka/marar lafiyar don shiga nazarin?

Ana yin wannan nazari ne don gano ko kwayar magani mai suna tranexamic acid tana kara sakamako bayan an sami raunin kai. An sanya ka (marar lafiya) ciki ne saboda ka sami mummunan rauni na kai wanda zai iya haddasa zubar jini cikin kwakwalwa. Kana (marar lafiya) daya daga cikin kusan marasa lafiya 13, 000 da ke da rauni na kai a fadin duniya da suke cikin wannan nazari.

## 3) Marar lafiya ba zai shiga cikin wannan nazari ba idan:

- likita yana ganin akwai wani dalili na musamman da ke cewa **kar a** bayar da tranexamic acid
- likita yana ganin akwai wani dalili na musamman da ke cewa **lalle a** bayar da da tranexamic acid
- Ita/shi ba baligi ba ne
- Ya/ta sami rauni sama da sa'o'I takwas kafin zuwa asibiti

## 4) Me shiga cikin wannan nazari ya kunsa?

An yi duk aiyukan gaggawa na rauni na kai da aka saba. Ba mu sani ko bayar da kwayar magani ta tranexamic acid akan duk sauran aiyukan bada maganin za ta taimaka ko a'a, don haka za a baiwa rabin marasa lafiya dake cikin nazarin tranexamic acid yayin da za a baiwa daya rabin wani maganin gwaji na bogi. Za a yi/an yi aikin bayar da maganin ne cikin sa'o'i takwas. An zabi abin da za a bayar ne (maganin gaske ko na bogi) ta hanyar canke (kamar gasar canke, kuma kai/marar lafiya zai sami cikakkiyar damar karbar kowanne daga ciki. Likitocin da ke kula da kai/marar lafiyar ba su san wanne daga cikin tranexamic acid ko maganin bogi aka ba ka ba. Babu bukatar a sake yi maka/marar lafiyar wasu karin gwaje gwaje ba ko kara zama a asibiti sakamakon shiga cikin wannan nazari. Aikin bada magani na nazarin kyauta ne.

## 5) Menene hatsarin kasancewa cikin nazarin?

Tranexamic acid ba sabon kwayar magani ba ne. An sha yin amfani da shi a tsawon shekaru don rage zubar jini bayan yin tiyata da kuma musamman kwanan nan don yin aiki ga sauran nau'o'I na rauni mai tsanani. Yana aiki ne ta hanyar tsayar da narkewar gudajin jini wadanda ake bukata don tsayar da zubar jini. Nazarin bincike da yawa sun nuna cewa ba ya haddasa daskarewar jini da ba a so sannan kuma babu wasu illoli masu karfi yayin amfani da shi na gajeren lokaci. Koda yake, likita zai lura da kai/marar lafiyar sosai sannan zai bada bayani ga masu shirya nazarin idan akwai wasu matsaloli na bazata.

## 6) Wadanne irin amfani za a samu ta shiga cikin nazarin?

Muna fatan cewa Tranexamic acid zai taimaka wajen rage zubar jini a cikin kai bayan an sami rauni a kai, wanda babban abu ne da ke haddasa mutuwa da nakasa bayan an ji rauni a kai. Ilimin da za mu karu da shi a wannan nazari zai taimakawa mutane masu irin wadannan raunuka nan gaba.

## 7) To idan kuma na ce na fasa shiga cikin nazarin fa?

Za ka iya janyewa daga cikin nazarin a kowane lokaci. Kawai za ka ce ne a misali *"Na yanke shawarar ba zan shiga wannan nazari ba yanzu."* Wannan ba zai shafi kulawar da za ka samu a wannan Asibiti ba. Muna fatan za ka bari mu yi amfani da bayanai game da yadda ka/marar lafiyar ke cigaba da rayuwa, amma idan ba ka son mu yi amfani da bayanan gaya wa likitan haka. Duk kan a dadin bayanan da ka samar daga cikin wannan bincike za'a yi amfani dashi. Tsarin kare dokoki na bayanai na UK a za'a ai'watar dashi yadda ya kamata.

## 8) Shin za a ajiye bayanin da ka karba a kebance?

Za a ajiye duk bayanai game da kai/marar lafiya da raunin a kebance. Mutanen kadai da aka baiwa damar duba bayanan sune likitocin da ke gudanar da nazarin da ma'aikata a Cibiyar Shirya Gwaji da ke LSHTM (Jami'ar Landan) da kuma hukumomin lura da bin ka'ida wadanda ke dubawa don tabbatar da ana gudanar da nazarin daidai. Likitanka zai aika da takaitattun bayanai game da kai/marar lafiya zuwa ga Cibiyar Shirya Gwaji da ke LSHTM. Mutanen da ke aiki a nazarin za su yi amfani da kebantattun bayan mutum ne cikin matukar sirri sannan kuma ba za a fitar da shi ba a cikin kowane irin hali. Za mu buga sakamakon nazarin a mujallar aikin likita don sauran likitoci su amfana daga ilimin, amma ba za a hada da kebantattun bayanan ka/na marar lafiyar ba don haka babu yadda za a gane ka/marar lafiyar.

Za a bayyanar da bayanai ba tare da an hada da kebantaccen bayanin mutum ba don amfanin sauran masu bincike da kuma jama'a.

Cibiyar Shirya Gwaji za ta iya neman tattara ko ta kwafi wasu takardun gwaji wadanda za su kunshi sunanka sannan kuma za su hada da Fom din Amincewa da aka sa-hannu. Wannan zai taimaka musu wajen tabbatar da cewa ana yin gwajin daidai.

## 9) Wa za ka/marar lafiyar zai tuntuba game da wasu tambayoyi ko matsaloli?

Idan kana da wasu tambayoyi ko damuwa game da kowane irin bangare na wannan nazari, sai ka nemi yin magana da likitocin nazarin wadanda za su yi matukar kokarinsu don amsa tambayoyinka. Dakta [shigar da suna] shi ne mai kula da wadannan nazari a wannan asibiti. Za ka iya tuntubar likitan a:

| | |
|---|---|
| Adireshi | |
| Tarho | |

Za ka iya tuntubar babban jami'in likita mai kula da wannan Asibiti ta wannan hanyar :

| | |
|---|---|
| Sunan datakta | |
| Adireshi | |
| Tarho | |

Idan har yanzu kana da damuwa kuma kana son yin karafi akai, za ka iya yin haka ta hanyar bin ka'id'jin korafi na asibitin. Tambayi masu bincike don samun cikakkun bayanai.

Likitoci da kuma kugiyar masu gwaji daga Makarantar Koyon Kiwon lafiya da Magunguna (LSHTM) da ke Jami'ar Landan ne suka shirya wannan nazari. Za'a iya tuntubar su ta wannan hanyar:

| | |
|---|---|
| Adireshi | CRASH-3 Trial Coordinating Centre, Lodnon School of Hygiene & Tropical Medicine, Room 180, Keppel Street, London WC1E 7HT, United Kingdom |
| Tarho | +44 20 7299 4684 |

## 10) Waye ya duba nazarin?

Don kare muradan ka, wani gungun mutane masu zaman kansu da ake kira Kwamitin Tabbatar da ka'idar Bincike ne suke duba duk wasu nazari da ake gudanarwa. Wannan nazari an duba shi kuma ya sami kyakkyawan bayanin cikar ka'ida daga Kwamitin Tabbatar da ka'idar Bincike a na wannan asibiti. Idan kana da wata tambaya akan hakkin ka, ko kuma kana jin vewa an tauye hakkin ka a matsayin ka na wanda ya shiga gwajin, to za'a iya tuntubar shugaba ta wannan adireshi:

| | |
|---|---|
| Sunan shugaba | |
| Adireshi | |

Haka kuma nazarin ya sami amincewa a Nijeriya daga:
*Daraktan sashen Kula da Yin rijista na Hukumar Kare lafiyar Abinci da Magunguna (NAFDAC)*
*445, Herbert Macaulay Way*
*Yaba, Lagos, Nigeria*
*Tarho: 01 477 2452*

## 11) Me zai faru bayan haka?

Za mu so mu ji idan ka/marar lafiyar ya sami wata matsalar lafiya bayan sallama daga wannan asibiti da kuma a kowane lokaci har zuwa kwanaki 28. Za a ba ka kati mai dauke da bayanan tuntuba na likitan bincike a wannan asibiti, wanda ya kamata ka adana shi a muhimmin waje da kuma mika shi ga duk wanda ke duba ka/marar lafiyar akan kowace cuta.

Idan kana son karbar kwafi na sakamakon karshe na wannan nazari, sanar da likitan bincike inda shi/ita kuma zai tabbata an ba ka kwafi lokacin da aka buga sakamakon. Za kuma ka iya ziyartar shafin intanet na gwajin don sanin yadda gwajin ke tafiya: **crash3.Lshtm.ac.uk**

## 12) Me kuma ka ke bukatar ka sani?

- Jami'ar Landan ce ta shirya nazarin inda kuma aka dauki nauyinsa da kudaden gwamnati da na tallafi, ba masu yin tranexamic acid ba.
- LSHTM {Jami'ar Landan} a matsayin masu shirya nazarin ta dauki alhakin nauyin da ke hade da daukar nauyin nazarin sannan, kamar haka, za ta dauki nau'yin neman diyyar kowace illa da duk wani mutum da ya
- Za mu nemi ka sa hannu a wani fom din amincewa daban sannan za a baka kwafi guda don ajiyewa haka nan za ka iya ajiye wannan takardar bayani.